| JUMHURIYYAR MISRA TA LARABAWA | 20 Jimada al- Ula, 1443 |
| --- | --- |
| MA'AIKATAR ADDININ MUSULUNCI | 24 Disamba, 2021 |

(١)

## SIFOFIN MUMINAI A CIKIN ALƘUR'ANI MAI GIRMA

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari suna da aljannatan da ƙoramu suke gudana ta ƙarƙashinsu, lallai wannan shi ne babban rabo)** [al- Buruj: 11], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai imani shi ne mafi girman ni'imomin da Allah Maɗaukakin Sarki yake yi wa mutum, Allah mai girma yana cewa: **(Hasali ma Allah ne yake da daman gorata maku saboda ya shiryatar da ku zuwa ga imani, in dai har ku masu gaskiya ne)** [al- Hujrat: 17], shi ne hanyar isa zuwa ga amintacciyar rayuwa mai cike da natsuwa, da samun nasara da babban lada, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Duk wanda ya aikata ayyuka na gari cikin maza da mata, yana cikin halin imani, to kuwa za mu raya shi rayuwa mai kyau, za kuma mu saka masu da ladansu sama da abin da suke aikatawa)** [an- Nahl: 97], haka ma mai girma da buwaya yana cewa: **(Lallai waɗanda suka yi imani da Allah, suka bi umurninsa, suke kuma aikata ayyuka na gari da ya umurta, suka bar haramun ɗin da ya hana, suka bayar da salloli a cike, suka kuma bayar da zakka ga waɗanda suka cancanta, suna da lada mai girma da yake ajiye a wajen Ubangijinsu, ba za su ji tsoro akan wani abu da zai zo nan gaba**

**ba, ba kuma za su yi baƙin-ciki akan abin da ya kuɓuce masu ba)** [al- Baƙra: 277].

Duk wanda ya yi wa Alƙur'ani mai girma kallo na tsanaki da lura, zai ga cewa lallai Allah mai girma da ɗaukaka ya sifanta muminai da sifofi masu yawa a cikin gagara gasan littafinsa, a cikin waɗannan sifofin akwai: Kiyaye sallah da bayar da ita a lokacinta, tare da cika rukunnanta, da kuma tsoron Allah, da ƙasƙantar masa da kai a ciki, Allah mai girma yana cewa: **(Lallai muminai sun sami babban rabo, su ne waɗanda suke tsoron Allah da ƙasƙantar da kai a cikin sallarsu)** [al- Muminun: 1 - 2], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Su ne waɗanda suke kiyaye sallolinsu)** [al- Muminun: 9].

A cikin waɗannan sifofin akwai: kawar da kai ga barin lagawu, sawa'un na magana ne ko na aiki, Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Su ne waɗanda suke kawar da kai ga barin lagawu)** [al- Muminun: 3], su muminai ba ruwansu da ƙananan abubuwan da suke gadar da ƙasƙanci, a koda yaushe suna mayar da hankula ne akan abubuwa masu girma da ma'ana, Allah mai girma yana cewa: **(Idan sun ji ana lagawu sai su kawar da kai ga barinsa)** [al- Ƙasasi: 55], haka ma yana cewa: **(Su ne waɗanda ba sa shaidar zur, idan sun wuce ta wurin da ake yin lagawu sai su tafi cikin karamarsu su wuce da sauri)** [al- Furƙan: 72], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(A cikin kyawon Musulunci mutum akwai ya bar abin da babu ruwansa).**

A cikin sifofin akwai: Ciyarwa, da bayar da umurni da aikata abubuwa masu kyau, da hana aikata munanan ayyuka, Allah mai girma yana cewa: **(Su ne waɗanda suke bayar da zakkarsu)** [al- Muminun: 4], haka mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Muminai**

**maza da mata dukansu masoyan juna ne, kuma masu taimakon juna; sakamakon imanin da suka yi, suna bayar da umurnin aikata abin da addininsu na gaskiya ya bayar da umurni, suna kuma hana aikata abubuwan da addini bai yarda a aikata ba, suna gabatar da sallah a lokutansu, suna kuma bayar da zakka ga waɗanda suka cancanta a lokutansu, suna kuma aikata abubuwan da Allah da Manzonsa suka bayar da umurnin a aikata, suna kuma nesantar abubuwan da Allah da Manzonsa suka hana, lallai waɗannan su ne inuwar rahamar Allah za ta mamaye su, lallai Allah mai iko ne akan ya lulluɓe su da rahama, mai kuma cikakkiyar hikima ne wajen baiwa, da kyaututtukansa)** [at- Tauba: 71].

A cikin waɗannan sifofin akwai: kasancewarsu cikin masu kamewa da tsantseni, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Su ne waɗanda suke kiyaye farjinsu, in ba akan matansu, da kuyangin da suka mallaka ba, akan waɗannan kam su ba abin zargi ba ne)** [al- Muminun: 5 -6], lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yakan roƙi Ubangijinsa kamewa a cikin addu'arsa, yana cewa: **(Ya Allah Ubangiji ina roƙon ka ba ni shiriya, da tsoron Allah, da kamewa, da wadata),** Muhammadu Bn Hanafiyya (Allah ya ƙara masa rahama) yana cewa: Kamala tana cikin abubuwa guda uku: kamewa a cikin addini, da haƙurin akan bala'o'i, da kuma kyautata tsuwurwurta a cikin rayuwa.

A cikin waɗannan sifofin akwai: Kiyaye amana, da cika alƙawari, shi mumini na haƙiƙa a koda yaushe yana renon sifar amana a tare da shi kaman yanda manomi yake renon shukarsa, da kaman yanda ma'aikaci yake renon sana'arsa, shi imani da cika alƙawari abubuwa ne da suke haɗe da juna, Allah mai girma yana cewa: **(Su ne waɗanda suke matuƙar kiyaye alƙawurransu)**

[al- Muminun: 8], Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ya ku waɗanda kuka yi imani, ku cika alƙawurran da kuka ƙulla)** [al-Ma'ida:1], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Lallai Allah yana ba ku umurnin ku mayar da amana ga masu ita)** [an-Nisa'i: 58], lallai Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya haɗe tsakanin amana da imani a inda yake cewa: **(Babu imani ga wanda ba shi da amana, haka ma babu addini ga wanda ba shi da alƙawari).**

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga fiyayyen halitta, shugabanmu Annabi Muhammadu da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

A cikin sifofin muminai akwai: kasancewarsu suna dawwama da ambaton Allah mai girma da buwaya, suna kuma kyautata dogara da shi (Subhanahu wa ta'ala), Allah mai girma yana cewa: **(Lallai waɗanda suka yi mani da Allah, zukatansu suka natsu da ambaton Allah, da ma can da ambaton Allah ne zukata suke natsuwa)** [ar- Ra'ad: 28], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Muminai su ne waɗanda idan aka ambaci Allah, sai zukatansu raurawa, idan kuma aka karanta masu ayoyinsa, sai karatun ya yi sanadiyya ƙaruwar imaninsu, su a koda yaushe suna dogara da Ubangijinsu ne)** [al- Anfal: 2], dogara da Allah na haƙiƙa shi ne bawa ya yi gaskiya wajen dogara da Allah Maɗaukaki, kuma hakan ba ya cika sai an haɗa da aiki da sababi na aiki da ijtihadi, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam yana cewa: (**Da za ku dogara da Allah kaman yanda ya kamata, da kuwa Allah ya azurta ku, kaman yanda yake azurta tsuntsu, yakan wayi gari cikinsa a ɗame, ya kuma yammanta a ƙoshe)**.

Shi imani na haƙiƙa shi ne wanda tasirinsa yake bayyana a cikin rayuwar al'umma, mumini na ainihi ba zai taɓa zama mai algushi ba, ba zai taɓa zama munafuki ba, ba zai taɓa zama maƙaryaci ba, ba zai taɓa zama mai saɓa alƙawari da ha'inci ba, ba zai taɓa zama mayaudari ba; saboda shi imani tsaftace zuciyar mai shi yake yi, shi mumini na ainihi rayayye ne, mai karamci, yana kusantar mutane, mutane ma suna kusantarsa, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Sannan ya kasance cikin waɗanda suka yi imaci, suka kuma yi wasici da yin haƙuri, suka kuma yi wasici da yin tausayi)** [al- Balad: 17], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Ina rantsuwa da zamani; saboda yawan abubuwan da ya ƙunsa** na **ban mamaki da lura. Lallai kowane mutum yana cikin wani nau'i na asara; saboda rinjayar da son zuciya da sha'awa da suka taru suka yi masa yawa. Sai dai ban da waɗanda suka yi imani da Allah, suka kuma aikata ayyuka na gari, suka kuma yi ɗã'a da biyayya, suka kuma yi wa juna wasici da riƙo da gaskiya wajen i'itiƙadi da furuci da aiki, suka kuma yi wa juna wasici da haƙuri akan abubuwa masu wahala da suke bijiro wa duk wani wanda ya yi riƙo da addini, waɗannan kam, su ne masu tsira daga wannan asara, masu kuma babban rabo a duniya da lahira)** [al- Asri: 1-3], Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to kada ya cutar da maƙwabcinsa, duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya girmama baƙonsa, duk wanda ya yi imani da Allah da ranar lahira, to ya faɗi alhairi ko ya yi shiru).**

Lallai akwai tsananin buƙatar a ce mun yi ado da karantarwar da imani yake yi mana, ta yanda za mu sami cikakken aminci da kwanciyar hankali da natsuwa, da jin daɗin duniya da lahira,

lallai Allah Maɗaukakin Sarki ya faɗi sakamakon muminai a inda yake cewa: **(Waɗannan su ne magada, waɗanda za su gaji aljannar Firdausi, za kuma su dawwama a cikinta)** [al- Muminun: 10 – 11], haka ma Allah mai girma yana cewa: **(Sai waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari, suna da lada ba mai yankewa ba)** [at- Tin: 6], haka ma Allah Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Lallai waɗanda suka yi imani, suka kuma aikata ayyuka na gari suna da aljannatan Firdausi a matsayin su ne masaukansu, za su dawwama a cikinsu, ba za su taɓa neman a sauya masu ba)** [al- Kahfi: 107 – 108].

**Ya Allah Ubangiji ina roƙon ka sanya mana son imani, ka ƙawata shi a cikin zukatanmu.**